*Wannan fassarar ƙungiyoyin Social Development Direct da Translators without Borders suka yi ta da manufar sanarwa kawai. BOND ba za su iya tabbatar da daidai din sa ba. Sigar da aka amince da ita kawai a hukumance ita ce wadda za'a iya samu a shafin yanar gizo na BOND [Safeguarding policy templates | Bond].'*

# Kiyayewa ta Bond
# Manufar Kiyayewa

## Dalilin

Dalilin wannan manufa shi ne don kare mutane, musamman yara, manya da masu cin gajiyar taimako da suke cikin haɗari, daga kowace cutarwa da za ta iya faruwa saboda haɗuwa da [NGO]. Wannan ya hada da illa da za ta iya tasowa daga:

- Halayen ma'aikatan ko ma'aikatan da suke da alaƙa da [NGO]
- Tsarawa da aiwatar da shirye-shirye na ayyukan [NGO]

Manufar tana bayyana alkawuran da [NGO] suka yi, kuma tana sanar da ma'aikata da ma'aikata masu alaƙa[1] akan daukar nauyinsu da ya danganci Kiyayewa.

Wannan manufa bata ƙunshi:

- Tursasawa ta fuskar jima'i a wajen aiki ba – an yi maganar wannan a karkashin Manufar [NGO] ta Hana Tsangwama da Tursasawa[2]
- Damuwa kan kiyayewa a cikin al'umma gaba daya wanda ba ma'aikatan [NGO] ko mai alhakin gudanarwa ya aikata ba

## Menene kiyayewa?

A Burtaniya, kiyayewa yana nufin kare lafiyar mutane, jin dadinsu da hakkokinsu, da kuma taimaka musu da yin rayuwa ba tare da illa, cin zarafi da sakaci ba[3]

A ɓangarenmu, mun fahimce shi yana nufin kare mutane, har da yara da manyan da suke cikin haɗari, daga illoli da suke tasowa daga haɗuwa da ma'aikatanmu ko shirye-shiryenmu.

Karin ma'anoni game da kiyayewa an ba da su a cikin kamus da yake ƙasa.

## Abubuwan da ya ƙunsa

- Dukkan ma'aikatan da [NGO] ta dauka kwangila

[1] Duba 'Abubuwan da ya ƙunsa don ma'anar mai alhakin gudanarwa
[2] Yanzu wasu NGOs suna hada tsangwama da tursasawa a wajen aiki cikin kundin hotunansu na Kiyayewa, bisa ga yadda yake da alaƙa da illa sakamakon haɗuwa da ma'aikatanmu ko shirye-shiryenmu. Amma hanyoyin da suke biyo baya don magance tsangwama da tursasawa a wajen aiki akwai yiwuwar za su bambanta, saboda banbancin buƙatun shari'ah wajen magance abubuwan da suke faruwa a wajen aiki
[3] NHS 'Menene kiyayewa? Mai saukin Karantawa' 2011

- Mai alhakin gudanarwa a lokacin da yake aiki ko ziyara da ta danganci [NGO], har da amma bai tsaya a waɗannan ba: kwararru ma su ba da shawara; ma su aikin sa kai; ‘’yan kwangila; masu ziyartar shirye-shirye har da ‘’yan jarida, shahararru da ‘’yan siyasa

# Bayanin Manufar

[NGO] sun amince cewa duk wandanda muka haɗu da su, ba tare da la'akari da shekaru, sanin jinsi, nakasa, ra'ayin jima'i ko asalin yare yana da hakkin samun kiyayewa daga dukkan nau'in illa, cin zarafi, sakaci da cutarwa ta ci da gumi. [NGO] ba za su amince da cin zarafi da ci da gumi daga ma'aikata ko mai alhakin gudanarwa ba.

Wannan manufa za ta magance waɗannan ɓangarorin kiyayewa [yadda ya dace]: kiyaye yara, kiyaye manya, da kiyayewa daga ci da gumi da cin zarafi ta fuskar jima'i. Waɗannan muhimman ɓangarorin kiyayewa watakila suna da manufofi da hanyoyin da suke alaƙa da su (duba Manufofi masu Alaƙa).

[NGO] ta yi alƙawarin kulawa da kiyayewa a dukkan ayyukansu, ta rukunnai uku na kiyayewa, kai rahoto da daukar mataki.

# Kariya

## Alhakin [NGO]

Aniyar [NGO]:

- Tabbatar dukkan ma'aikata za su samu dama, su saba da, kuma su san nauyin da ke kansu game da wannan manufar
- Tsara da aiwatar da dukkan shirye-shiryensu da ayyukansu ta hanyar da zai kare mutane daga kowane haɗarin illa da zai iya tasowa sakamakon haɗuwa da [NGO]. Wannan ya hada da hanyar da ake tattara bayanai game da ɗai-ɗaikun mutane a cikin shirye-shiryenmu da kuma sadar da su
- Aiwatar da hanyoyin kiyayewa masu tsaurii a lokacin ɗaukan ma’aikata, gudanarwa da rarraba ma'aikata da ma'aikata masu alaƙa
- Tabbatar ma'aikata sun samu horo akan kiyayewa a wani matakin da ya dace da matsayinsu a cikin ƙungiyar
- Bibiyar rahotannin damuwa kan kiyayewa da wuri kuma bisa hanyar da ta dace

## Alhakin ma'aikata

**Kiyayewar Yara**

Ma'aikatan [NGO] da ma'aikata masu alaƙa dole kar su:

- Yi jima'i da kowa wanda yake ƙasa da shekaru 18
- Ci zarafi ko ci da gumi akan yara ta fuskar jima'i
- Ci zarafin yaro/yarinya a zahiri, ta shauki ko tunani, ko sakaci
- Yi kowane ayyukan kasuwanci ta ci da gumi akan yara har da bautar da yaro/yarinya ko fataucinsu

**Kiyayewar Manya**

Ma'aikatan [NGO] da ma'aikata masu alaƙa dole kar su:

- Ci zarafi ko ci da gumi akan manyan da suke cikin haɗari ta fuskar jima'i
- Sa babba dake fuskantar hadari cikin cin zarafin zahiri, ta shauki ko tunani, ko sakaci

**Kiyayewa daga ci da gumi da cin zarafi ta fuskar jima'i**

Ma'aikatan [NGO] da ma'aikata masu alaƙa dole kar su:

- Musaya da kuɗi, aiki, kaya, ko hidimomi don aikata jima'i. Wannan ya hada da kowace musayar taimako da ya kamata ma su cin gajiyar su samu
- Shiga kowace dangantakar jimai da masu cin gajiyar taimako, tunda sun dangantu da yadda iko ke shafar dangantaka

Bugu da ƙari, ya zama wajibi ma'aikatan [NGO] da ma'aikata masu alaƙa su:

- Ba da gudunmawa wajen samarwa da lura da wani muhalli wanda yake hana sabawa ka'idojin kiyayewa kuma ya karfafawa aiwatar da Manufar kiyayewa
- Kai rahoton kowace damuwa ko zarge-zarge game da sabawa ka'idojin kiyayewa daga ma'aikatan [NGO] ko ma'aikata masu alaƙa zuwa ma'aikacin da ya dace

# Taimakawa rahotanni

[NGO] za su tabbatar cewa an samar da hanyoyin karɓar rahotannin damuwar kiyayewa masu aminci, wandanda suka dace kuma suna samuwa ga ma'aikata da al'umma da muke aiki da su.

Kowane ma'aikacin da yake kai ƙarar damuwa ko korafe-korafe ta hanyoyin fallasa da aka amince da su (ko idan sun bukace shi) zai samu kiyayewa ta Manufar [NGO] ta Bayyana Rashin Da'a a Wajen Aiki (Manufa kan Fallasa).

[NGO] za su iya karbar korafe-korafe daga waje kamar daga jama'a, abokan aiki da hukumomin ƙasar.

**Yadda za'a kai rahoton damuwa kan kiyayewa**

Ma'aikatan da suke da korafi ko damuwa game da kiyayewa ya kamata su kai rahoton nan take zuwa Masu Jagorantar kiyayewa [yadda ya dace] ko manajan bangare. Idan ma'aikacin yana tsoron kai rahoton ga Masu Jagorantar kiyayewa ko manajansa (misali idan suna ganin cewa ba za'a ɗauki rahoton da mahimmanci ba, ko idan damuwar ta shafi mutumin) za su iya kai ƙarar zuwa wani ma'aikaci daban da ya dace. Misali, wannan na iya zama babban manaja ko wani ma'aikaci daga ɓangaren HR.

[Ba da bayanin tuntuba]

# Tallafawa

[NGO] za su yi bibiyar rahotannin kiyayewa da damuwa bisa ga manufa da hanyar, da kuma buƙatun shari'ah (duba Hanyoyin karɓar rahoto da daukar mataki kan damuwa da kiyayewa a Manufofi masu Alaƙa).

[NGO] za su aiwatar da matakan ladabtarwa da ya dace ga ma'aikatan da suka sabawa Manufar.

[NGO] za su ba da taimako ga wadanda suka tsira daga illar da ma'aikatan ko ma'aikata masu alaƙa suka jawo, ba tare da la'akari da ko an ɗauki matakin magancewa na cikin gida ba (kamar bincike na cikin gida). Shawarwarin da za a yanke game da taimako, wanda ya tsira ne zai jagoranta.

# Tsare sirri

Yana da matukar mahimmanci cewa an tabbatar da tsare sirri a dukkan matakai da ake bi a lokacin magance damuwar kiyayewa. Bayani game da damuwar da kuma magance ta daga baya ya kamata ya zama an yada bisa buƙatar a sani kawai, kuma ya kamata a kiyaye shi a dukkan lokuta.

### Manufofi masu alaƙa

Dokokin Aiki

Manufar Hana Tsangwama da Tursasawa

Manufar Bayyana Rashin Da'a a Wajen aiki (fallasa)

Ka'idar Kare Yara

Ka'idar Kare Manya

Manufar PSEA (Kiyayewa daga ci da gumi da Cin Zarafi ta Fuskar Jima'i daga ma'aikata)

Manufar Korafe-korafe

Hanyoyin karɓar rahoto da tallafawa ga damuwar kiyayewa

Hanyoyin kiyayewa a lokacin ɗaukar ma'aikata

Sauran manufofi yadda ya dace

# Kamus na Bayanai

**Masu cin Gajiyar Taimako**

Wanda ke karɓar kaya kai tsaye ko hidimomi daga shirin [NGO]. Lura cewa amfani da iko yadda bai kamata ba na iya shafar al'ummar da NGO ke taimakawa gaba daya, kuma yana iya hadar da amfani da dama ta nuna cewa sun fi matsayin iko.

**Yaro/Yarinya**

Mutumin dake ƙasa da shekaru 18

**Illa**

Kwaƙwalwa da tunani, zahiri da sauran hanyoyin take hakkin wani

**Illa da ta shafi ƙwaƙwalwa**

Cin zarafi da ya shafi ƙwaƙwalwa ko tunani har da (amma bai tsaya a) kaskantarwa da rashin mutunci kamar kiran sunan da ba'a so, yawan suka, raini, yawan kunyatawa da tsarewa da warewa ba

**Kiyayewa daga ci da gumi da Cin zarafi ta Fuskar Jima'i (PSEA)**

Kalmar da al'ummar taimakon agaji da ci-gaba suke amfani da ita da ke nufin hana ci da gumi da cin zarafin jama'ar da abun ya shafa ta fuskar jima'i daga ma'aikata da ma'aikata masu alaƙa. An samu kalmar ne daga Mujallar Babban Sakataren Majalisar Ɗinkin Duniya akan Matakai na Musamman don Kiyayewa daga ci da gumi da Cin Zarafi ta fuskar Jima'i (ST/SGB/2003/13)

**Kiyayewa**

A Burtaniya, kiyayewa yana nufin kare lafiyar mutane, jin dadinsu da hakkokinsu, da kuma taimaka musu da yin rayuwa ba tare da illa, cin zarafi da sakaci ba[4]

A ɓangarenmu, mun fahimce shi yana nufin kare mutane, har da yara da manyan da suke cikin haɗari, daga illoli da suke tasowa daga haɗuwa da ma'aikatanmu ko shirye-shiryenmu. Wata ma'anar ta mai ba da kuɗin tallafi ita ce kamar haka:

Kiyayewa tana nufin ɗaukan dukkan matakan da suka dace don hana ci da gumi ta fuskar jima'i, cin zarafi da tursasawa da nufin jima'i daga faruwa; don kare mutane, musamman manyan da suke cikin haɗari da yara, daga waccan illar; da kuma don ba da taimakon da ya dace idan illar ta faru.

Wannan ma'anar an tsamota daga al'ada da dabi'unmu. Yana mayar da hankali kan hana da daukar mataki kan illoli daga ƙoƙarin ko ainihin nuna iko, amfani da aminci, ko yanayin raunii, musamman don dalilin jima'i.

Kiyayewa ko yaushe ya shafi kuma ba tare da ware komai na shirye-shiryenmu, abokan aiki da ma'aikata ba. Yana buƙatar gano, hana da ba da kiyayewa da wuri daga dukkan hatsarorin illa, cutarwa ta ci da gumi da cin zarafi da kuma samar da tsarurruka na dattako, a bayyane na ɗaukan alhaki don tallafawa, kai rahoto da koyo idan hadurra sun bayyana. Waɗancan tsarurrukan dole su fuskanci-wanda ya tsira kuma su kare waɗanda ake zargi sai an tabbatar da laifinsu.

Kiyayewa tana sa masu cin gajiya da mutanen da abin ya shafa a tsakiyar dukkan abun da muke yi.

**Cin zarafi ta hanyar jima'i**

Hakan kuma, kalmar "cin zarafi ta fuskar jima'i" tana nufin ainihin ko barazanar zahiri ta fuskar jima'i, ko ta tilastawa ko kuma a yanayin rashin daidaito ko fin ƙarfi.

**Ci da gumi ta fuskar jima'i**

Kalmar "ci da gumi ta fuskar jima'i" tana nufin kowane ainihin cin zarafi da aka aikata ko ƙoƙarin aikatawa ta amfani da matsayin rauni, banbancin iko, ko aminci, don dalilin jima'i, har da, amma, basu tsaya ga, samun riba ta kuɗi, matsayi ko siyasa daga cutar da wani ta ci da gumi ta hanyar jima'i ba. Wannan ma'anar ta hada da fataucin mutane da bautarwa ta zamani.

**Wanda ya tsira**

Mutumin da aka ci zarafinsa ko cutar da shi ta ci da gumi. Kalmar ''wanda ya tsira" galibi an fi amfani da ita maimakon ''wanda abun ya shafa" saboda tana nuna ƙarfi, juriya da ikon tsira, amma zaɓin mutumin ne yadda suke so a kira su.

**Manyan da ka iya shiga cikin haɗari**

Wasu lokuta kuma ana kiran shi babba da ke da rauni. Mutumin da ko ke da buƙatar kulawa saboda dalilin nakasa da ya shafi ƙwaƙwalwa ko wata nakasar, shekaru ko rashin lafiya; kuma wanda ko watakil ba zai iya kulawa da kansa ko kanta ba, ko ba zai iya kare kansa ko kanta ba daga wata babbar illa ko cutarwa ta ci da gumi ba.

[4] NHS 'Menene kiyayewa? Mai sauƙin Karantawa' 2011